
# 'Yancin Mata a yanar gizo: Cike giɓin jinsi a dijital don samun daidaito a duniya



WORLD WIDE WEB
FOUNDATION

# 'Yancin Mata a yanar gizo: Cike giɓin jinsi a dijital don samun daidaito a duniya

Oktoba, 2020. Web Foundation

An daɗe ana amfani da yanar gizo a matsayin wata kafa ta haɓaka daidaito - kawar da shingen da ya hana cigaba musamman waɗanda yanayin ƙasa, dukiya, launin fata, matsayi a rayuwa da jinsi suka jawo. Ko ta yaya rashin daidaito na dogon lokaci game da samun damar shiga ko amfani da yanar gizo yana da alhaki wajen kawo rashin daidaiton jinsi.

Wannan rahoto ya ba wa duniya damar gano yadda yanayin rashin daidaiton jinsi, har ya fahimtar da cewa ko a wajen da mata suke cike gibin da ake da shi ta hanyar amfani da intanet, suna fuskantar tarin matsaloli da yawa a wajen amfani da intanet da shiga yanar gizo gaba daya.

Dangane da kungiyoyin da aka maida hankali akai, an samu damar tattaunawa da kuma binciken mata da maza kusan 10,000 a ƙasashe hudu - Colombia, Ghana, Indonesia da Uganda - rahoton ya yi nazari a kan waɗannan banbancin jinsi na dijital, inda binciken ya wuce kan masu amfani da intanet karo na farko zuwa duba kyawun intanet ɗin da damar da mutane ke da ita ta amfani da intanet, da irin matsalolin da ake fuskanta wajen samun damar shiga intanet.

Mahimman bincike

- *Samun sakamako mai gamsarwa kan samun damar amfani da intanet*: Uku daga cikin kasashe hudun da aka yi nazari akan su, sun sami karancin bambancin jinsi a wajen samun damar amfani da intanet, kodayake a Yuganda maza sun kasance sun fi mata da kusan kashi 43% a intanet. [Bayanai](#) sun nuna cewa a duk duniya maza sun kasance sun fi mata da kashi 21% cikin masu yiwuwar amfani da yanar gizo, inda ya haura zuwa 52% a cikin ƙasashe masu ci gaba.

- *Ɓoyayyen rabe-raben bambancin jinsi wajen zama dijital*: Amfani da yadda ake samun [haɗin intanet mai ma'ana](#) a matsayin cikakken ma'aunin ingancin samun dama - la'akari da saurin gudun shafin yanar gizo, yawan wajen adana bayanai, nau'in na'urar da samun dama ta yau da kullun - an samun giɓin jinsi mai yawa. A cikin Colombia, wadda ke da tazarar 1% na jinsi wajen samun damar shiga ta asali, ana samun tazarar kashi 17%.

- *Basira tana zama shinge wajen samun damar shiga*: Rashin ƙwarewar aiki ya zama babban abin da ke hana mata shiga yanar gizo. Kashi 50% na mata a yankunan karkara sun ce ba sa amfani da intanet ne saboda ba su san yadda ake amfani da shi ba.Yayin da kashi 45% na mata a cikin birane ma suke iƙirarin hakan

- *Rashin fasaha na daga cikin abubuwan da ke zama shinge wajen bawa mata damar zama dijital*. Rashin fasaha babban shinge ne ga matan. Kashi 50% na matan karkara sun tabbatar basa amfani da yanar gizo saboda basu yadda ake amfani da ita ba. 45% na mata a birane ma sun tabbatar da hakan.

- *Mata na ƙirƙirar mafi ƙaramin abu*: Lokacin da mata suka sami damar shiga yanar gizo, za'a ga basu da wani abu da suke ƙirƙira. Maza sun fi mata da kashi 29 cikin ɗari wajen yin tsokaci game da lamuran siyasa, zamantakewa ko tattalin arziki. Sannan kashi 29% na sayar ko tallata wani abu ko wani aiki ta yanar gizo.

- *Damuwa da kiyaye sirri.* Cikin bayanan wasu nau'in mata da aka tara, mata sun nuna muhimmancin kiyaye sirrinsu fiye da maza. Mahalarta taron sun gabatar da damuwar su game da cin zarafin bayanan su, wanda ya haɗa da tozarta su ko cin zarafin su.

- *Rashin amincewa da kamfanunnukan yanar gizo*. Mata kuma sun kasance masu shakku game da kamfanonin fasaha wajen tsoron ko zasuyi amfani da bayanan su yadda ya kamata. 54% na mata da su ka bada amsa sun ce ba za su ƙyale kamfanunnuka su yi amfani da duk wani bayanansu ba, idan aka kwatanta da kashi 47% na maza.

Cike gibin jinsi na dijital don daidaitawar duniya.

Tilas ana buƙatar hanzarta cike giɓin bambancin jinsi na dijital, a kuma tabbatar cewa mata da yammata za su iya shiga a dama da su ta yanar gizo ba tare da tsoron lafiya ko haƙƙin su ba. Har sai mun yi haka ne zai zama cewa intanet bai kawo tsaiko ba wajen cigaban daidaiton jinsi.

Fasahar dijital ba za ta ƙarfafawa mutane masu nuna wariya ba, wanda hakan zai sa ta saɓawa tsarin gargajiya ba tare da saka hannun jari na dogon lokaci ba da da jajircewar wajen shawo kan rashin daidaiton da ke akwai ta yanar gizo. Wannan rahoton ya nuna mahimman wurare, tare da matakai, waɗanda gwamnatoci da kamfanoni dole ne su mai da hankali akai don ba da dama da daidaituwar jinsi a duniyar digital.:

- Tattara da buga bayanan jinsi a ɓangaren fasaha
- Tabbatuwar haɗuwa mai muhimmanci akan amfani da yanar gizo don cike giɓin banbancin jinsi
- Inganta ƙwarewa a zama dijital da ilimin na'ura mai ƙwaƙwalwa ga manyan mata da kuma 'yammata.
- Marawa shigar mata cikin ci gaban fasaha, ƙirƙirar abubuwan cikin gida da ƙwarewar na'ura mai ƙwaƙwalwa baya.
- Kare bayanan sirri na manyan mata da 'yammata

Don ganin cikakken sakamakon binciken da cikakkun shawarwarin akanmanufofi, karanta rahoton da aka tara daga duk duniya.

Rahoton zane-zane daga Karen Vermeulen.
Fassarar Hausa daga Fatumah Batula. Radio Nigeria, Lagos
Nazarin harshen Hausa na Sadya Abba Gambo